# DIMOKURAƊIYYA TA YUNKURO A KASAR AFGHANISTAN

In ji
Colin Powell
Sakataren Harkoƙin Ƙasashen Waje na Amirka

A ranar 9 ga watan Oktoba, miliyoyin 'yan ƙasar Afghanistan za su jefa ƙuri'a domin zaɓen shuganban ƙasar su da zai ja ragama na tsawon shekaru biyar masu zuwa. Bayan an kwashe wata guda ana kanfe da kuma shirye-shirye, jama'ar ƙasar Afghanistan daga ko'ina da ma waɗanda ke gudun hijira a makwabtan ƙasashen Pakistan da Iran za su zaɓi mutum guda tsakanin 'yan takara 18 da ke neman shugabancin ƙasar. A karo na farko cikin tarihin su jama'ar Afghanistan za su zaɓi shugaban ƙasa ta hanyar jefa ƙuri'a a asirce, kuma a ƙarƙashin wani tsari da ke da goyon bayan duniya baki ɗaya.

Cikin shekaru huɗu da suka wuce, indan an ce wannan al'amari na zaɓe zai yiwu, mutane da dama zasu ɗauka mafarki ne. A wancan lokaci na baya, 'yan Taliban ne, waɗanda ba sa son wata adawa ke kankane da mulki, kuma suna amfani da shi mulkin wajen take hakkin jama'a, musamman ma mata, waɗanda basu da wani 'yancin yin kataɓus. An hana yara da mata zuwa makaranta, kana tattalin arzikin ƙasar da cibiyoyin tallafawa rayuwar yau da kullum, kamar asibitoci da makarantu, sun tsaya cik.

Amma a yau babu 'yan Taliban, kuma jama'ar Afghanistan na da wata muhinmiyar damar su chanza rayuwar su. Wannan damar kuwa, sakamakon aiki tuƙuru ne na jama'ar ƙasar da kuma taimakon Majalaisar Ɗinkin Duniya da ma ƙasashe da dama ƙawayen ƙasar ta Afghanistan. Wannan dama ce ga mutanen Afghanistan domin su yanke hukunci kan makoman ƙasar su.

An yi gagarumin shiri domin wannan zaɓe, akwai tasosin jefa ƙuria'a dubu huɗu da ɗari tara a faɗin ƙasar, kana hukumomin yankuna zasu saurari dukkan kokekoken maguɗi ko rashin bin ka'ida. Za'a faɗi dukkan sakamakon zaɓuɓɓukan ne a tasosin zaɓe, kuma a gaban wakilan 'yan takara, daga nan kuma za'a kai wannan sakamako ga hukumar zaɓe ta ƙasar da zata bayyana kammalallen sakamako na ƙasa baki ɗaya. Duk wannan tsari za'a gudanar da shi ne akan idon 'yan kallo na cikin gida da kuma na ƙasashen waje.

Wannan zaɓe yana da matuƙan muhinmanci, kuma za'a aiwatar dashi a matsayin ɓangaren wani shiri na ba gudu ba ja da baya. A shekaru biyu da suka gabata, jama'ar Afghanistan sun haɗa kansu domin samar wa ƙasar al'kiɓlan siyasa. Muna iya tuna taro da kuma yarjejeniyar Bonn na kafa gwamnatin Wucin Gaɗi da majalisar wucin gaɗi da ake kira Loya Jirga da kuma ƙaddamar da Majalisar Tsarin Mulkin Loya Jirga. A bazara mai zuwa ma za'a cigaba da ɗaukan muhimman matakai, kamar zaɓen Majalisar Dokoki, wanda za'a biyo bayansa da ƙaddamar da majalisar. Duk waɗannan shirye-shirye ne da zasu ƙarfafa dimoƙuraɗiyya su kuma inganta inganta madafan iko da cibiyoyin hukuma.

Tareda taimakon ƙasa da ƙasa, gwamnatin Afghanistan ta fara ƙoƙarin kafa dimoƙurɗiyya a yankuna karkara. Shugabanni na karfafa gwiwar jama'ar su domin su ɓullo da ƙungiyoyi a ƙauyuka da yankunan hakimai domin su zama tubalin gina tsarin mulkin dimoƙuraɗiyya mai ɗorewa. Wannan yunƙurin da ake yi zai samu nasarar haɗe jama'a wuri guda ta hanyar tattaunawa da yarda da juna.

Zai ɗauki lokaci kafin a gina cibiyoyin mulki da ake bukata domin gudanar da ƙasa mai tasowa, kuma a ilmantar da al'umanta domin su rungumin ɗabi'un siyasa na sanin muhimmancin 'yancin kai da bada goyon baya ga tabbatar da tsarin dimoƙuraɗiyya da mulki mai adalci. Amma ƙasar ta Afghanistan na da muhimmin abinda ake bukata domin samun nasarar wannan aiki na ginin ƙasa, watau dagewa da kuma sha'awan jama'ar ta na mulkin kansu da kansu, bayan an yi tsawon lokaci a na yaƙi da lalata ƙasar. Babban abinda yake nuna mana wannan sha'awa shine yadda miliyoyin 'yan Afghanistan ke takowa a kafa daga wurare masu nisa domin su zo rumfunan zaɓe su yi rijista. Suna hakan ne kuwa duk da barazana da burburshin 'yan Taliban ke yi na halaka su. Babu wani sha'awa na 'yancin kai da ya fi wannan.

Lokacin da 'yan Taliban suka kai hari wa jami'an zaɓe, jama'ar ƙasar Afghanistan sun maida martani ta hanyar zaƙulo maharan cikin gaggawa. Da aka sace wata motar safa ɗauke da mutane da suke rijista aka kuma musu kisan gilla, jama'ar ƙasar sun sake maida martani ta fitowa domin yin rijista. Yayinda kuma gwamnatin Afghanistan ta nemi taimakon ƙasa da ƙasa domin ƙarin tsaro a yankunan ƙasar da ke fama da tashe-tashen hankali, ƙasashe sun bada wannan taimako. Irin wannan haɗin kai ya na bukutar goyon baya, don haka ne Amirka da ƙawayenta ke bada goyon baya da ya kamata.

A yanzu haka akwai sojojin ƙawance dubu goma sha takwas da kuma sojojin Haɗin Kan Kas ashen Turai, watau NATO dubu tara a ƙasar Afghanistan. Akwai ma wadansu sojojin cikin shirin ko ta kwana, idan bukutar haka ta taso. Majalisar Ɗinkin Duniya da ƙungiyoyi masu zaman kansu da sauran ƙungiyoyi masu bada gudumawa sun taimaka kwarai wajen aikin rijista da kuma shirin zaɓen na Afghanistan baki ɗaya. A garin Berlin na ƙasar Jamus a watan Afrilu da kuma a taron Majalisar Ɗinkin Duniya na wannan shekara, shugabanni da ƙasashen duniya da dama sun tabbatar da goyon bayansu ga jama'ar Afghanistan.

Kamar yanda shugaba Bush ya jaddada ne, babban jarin 'yancin kai sune hakurin zama da juna da bin doka da kuma kare 'yancin jama'a na walwala. A Afghanistan, Amirka na goyon bayan gwamnatin farar hula kuma yarjejiniyar Bonn da shirye-shiryen ƙarfafa tsaro sune tubalin gina ƙasaer Afghanistan nan gaba. Idan mu da sauran ƙawayen Afghanistan muka dage kan wannan tsari, ƙasar za ta ginu kan turbar dimokuraɗiyya, a matsayin ƙasa mai riƙe da al'adunta na Islama, kuma babban abokin dogaro a yaƙi da ake yi da ta'addanci.